# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da



# Mutumi mai Wuta

**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Lazarus**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: E. Frischbutter**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**

Kome ya kasance mummuna wa Isra'ila. Sarki da sarauniya sun ki Allah. Mummunan misali! Ba a ddde ba mutanen su ma suka ki Allah suka yi wa allolin karya sujada. Akwai wanda ya kaunaci Allah? I'I, akwai 'yan raguwa masu sujada cikin aminci. Wata rana, Allah ya yi magana da dayansu, mai suna Iliya.



**Iliya ya gaya wa mugun Sarki Ahab, “Muddin Ubangiji Allahn Isra’ila yana da rai, ba za a sami raba ko ruwan sama a wannan shekaru ba, sai na furta kalmarta.” Wannan ya nuna yunwa mai tsanani! Allah ba zai bar mutanensa Isra’ila su ci gaba da muguntansu ba.**





Bayan da aka ja wa sarki kunne, Allah ya aike Iliya zuwa wani wuri marar surutu a bayan gari. A wurin, ta rafi, Iliya ya jira. Allah ya aika da hankaki domin su ciyar da shi. Suka kawo masa burodi da nama, da safe da yamma. Iliya ya sha ruwa daga rafin.



**Ba a dadde ba sai rafin ya bushe, saboda ba a yi ruwan sama ba a kasar. Kalmar Allah ta zama gaskiya. Duka kasar ta yi rashin ruwa. Hatsin ba su yi girma ba. Mutane suna jin yunwa. Watakila Iliya ya tunani ko mene ne zai faru da shi yanzu da ruwan ya kare.**

Allah ya gaya wa Iliya, “Tashi, tafi wurin Zarafet, ka zauna a wurin.  Duba, na riga na umarta wata gwauruwa ta ciyar da kai.”  Allah ya san bukatun bawansa. Amma don me ya zamaba iri wannan hanyar tanadawa.  Cikin tawaliyu, Iliya ya yi biyayya ga Allah. Sa’ad da ya kai Zarafet, gwauruwar tana a bakin kofar birnin tana tattara kara don itacen wuta.



“Ina roko ki dan kawo mini dan ruwa a kofi,” Iliya ya roke matan. “Ina roko, ki kuma kawo mini dunkulen burodi.” “Ba ni da burodi,” gwauruwar ta amsa. “Garin filawan da nake da shi kunshin hannu ne da kuma dan karamin mai a gora.”



Abin bakin ciki, macen ta fada wa annabin cewa idan wannan ya kare, da ita da danta za su yi tsananin yunwa har mutuwa.

**“Kada ki ji tsoro. Ke dai ki yi mini dan gurasa da shi, bayan haka sai ki naki da ke da yaronki.” Iliya ya ce. “Wannan garin filawa ba zai kare ba, kuma mai din ba zai kare ba, har sai ranar da UBANGIJI ya aiko da ruwan sama a duniya.” Ai sai da al’ajibin Allah kafin wannan ya faru. Kuma ya yi! Matan da yaronta suka ci na kwanaki masu yawa, amma duk da haka garin filawan bai kare ba, ko mai din ya kare.**



**Iliya ya zauna da su. Wata rana wani abin bakin ciki ya faru. Yaron gwauruwan ya mutu. Iliya dauka jikin yaron zuwa daki na sama. Sai ya yi kuka ga UBANGIJI,**



**yana cewa, "Ya UBANGIJI Allahna ina roko, bari ran yaron nan ya dawo gareshi." Addu'ar da zai iya faru ba!**

UBANGIJI ya ji muryar Iliya sai ran yaron ya dawo gareshi, sai ya tsira. Sa’ad da Iliya ya dauki yaron zuwa wurin uwarsa, sai uwar ta ce, “Yanzu ta wurin wannan, na sani cewa kalmar UBANGIJI a bakinka shi ne gaskiya.”



**Bayan shekaru uku, Allah ya aike Iliya zuwa wurin sarkin, yana cewa, “Zan aiko da ruwan sama a kasa.”  Je wurin Ahab?  Matarsa Yezebel ta riga ta kashe annabawa dari na Allah.  Amma Iliya bai yi muhawwara ba.**
**Ya tafi wurin sarki Ahab.**



Sa’ad da maza biyun suka sadu, Iliya ya kalubalance Ahab ya tattara duka Isra’ila da annabawan karya guda 850.  A wurin da ake kira  Tuddun Kamel, Iliya ya yi magana da mutanen.  “Idan UBANGIJI Allah ne, ku bi shi.”



**Iliya ya sa aka shirya bijimai biyu na hadaya. Amma ba za a yi amfani da wuta don a kona su ba. “Ku kira ga suna allolinku, ni zan kira ga sunan UBANGIJI.” ya ce. “Kuma duk allhahn da ya amsa ta wurin wuta, shi ne Allah.” “Maganarka daidai ne,” mutanen suka amsa.**



**Daga safe zuwa yamma annabawan karyan sun yi ta kira ga allolin karyansu. Suna tsalle suna rawa suna yayyanka jikunansu da wukake har jini ya fita. Amma babu wutan da ya fita.**





**Sai Iliya ya jika itacen da abin hadayar da ruwa ya yi addu'a. "Ya UBANGIJI, ji ni, don wadannan mutane su sani kai ne UBANGIJI Allah…" Sai wutan UBANGIJI ya fadi. Ya kone bijimin da itacen. Sai ya kone duwatsun bagaden.**

Sa’ad da mutane suka gan shi, suka yi kuka, “UBANGIJI, shi ne Allah!”  Iliya ya ce, “Ku kakkama annabawan Baal.  Kada ku bar ko dayansu ya kubce!”  Iliya ya yi abin da yakamata Sarki Ahab ya yi tun tuni.  Ya kakkashe annaban karyan.



**Sai ‘yan hidimar Allah suka gaya wa Ahab cewa ruwan sama yana a hanya. Ba a dadde ba sai aka ga dan hadari ya bayyana. Ko za a yi ruwan sama? Bayan shekaru uku da**

**ruwa bai sauka ba?**





**A dan lokaci kadan, sai sararin sama ya fara zama baki da hadari da isak, sai ga ruwan sama mai yawa.  Allah ya aikar da ruwan sama. Allah ya nuna wa mutanensa cewa Iliya yana gay musu gaskiya ne.  Allah ya nuna cewa shi ne kadai Allah na gaske.**



A tunaninka kana gani kamar Sarki Ahab ya daukaka Allah da bawansa Iliya? A'a! Gaskiyar ita ce, Yezebel ta yi kokari ta kashe Iliya, amma ya tsira. A karshe, Ahab ya mutu a bakin daga sai 'yan hidimarsa suka tura Yezebel daga bangon gidan sama na gidan sarkin. Ta gangara kasa tana bubbuga jiki a kan duwatsun har ta mutu.



**Mene ne ya faru da Iliya? Wata rana Allah ya aiko da keken doki na wuta da dawaki; kuma Iliya, mutumin Allah mai wuta ya haura sama cikin gugguwa.**

# Mutumi mai Wuta

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**1 Sarakuna 17-19,**
**2 Sarakuna 2**

**"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130**

# KARSHE

24

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin**
**Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**